The Kumbotso Teacher Educator (KUTEJ):
A Journal of Multidisciplinary Studies
Vol 6.2 July 2016 ISSN: 1597-8796

# NAZARIN SALON AMFANI DA TAURARI A MATSAYIN GINSHIQAN RUBUTA QAGAGGUN LABARAI NA HAUSA: TSOKACI A KAN LITTAFIN *JIKI MAGAYI*

***Umar Yahaya***
Sashen Koyar da Hausa
Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kumbotso, Jihar Kano

## Tsakure

Samar da taurari a aikin bayar da labari ginshiqi ne wajen isar da saqo. Cim ma manufar marubucin qagaggen labari ya dogara da salon amfani da taurarinsa, domin kuwa su ne waxanda yake amfani da su ya sakar musu aikin bayar da labari su riqa magana a maimakonsa, ma'ana dai su ne suke arar bakin mawallafi su ci masa albasa. Wannan takarda an xora ta ne a kan Ra'in Dabarun Bayar da Labari da Mukhtar (2004) ya samar a cikin littafinsa mai suna *Jagoran Nazarin Qagaggun Labarai* a inda aka kalli yadda marubutan littafin *Jiki Magayi* suka yi amfani da taurarin cikin labarinsu ta bayyana sigar taurarin da rukunan ajin da suka faxa da yadda suke aiwatar da lamuransu a cikin labarin. Manufar takardar ita ce ta nazarci salon da marubutan suka yi amfani da shi wajen zavin taurarinsu domin su isar da

saqonsu ga al’umma. An kasa takardar ce gida uku, kashi na farko ya qunshi gabatarwa da waiwaye kan ra’ayoyin masana game da salo, sannan taurari da nau’o’insu. Kashi na biyu kuma, ya qunshi salon da marubutan suka yi amfani da shi wajen zavin taurarinsu a littafinsu na *Jiki Magayi*. Kashi na qarshe kuwa ya qunshi jawabin kammalawa. Sannan aka taqaita sakamakon bincike, sai kuma manazarta ta biyo baya.

## 1.0 Gabatarwa

Salon amfani da taurari a aikin bayar da labari ginshiqi ne wajen isar da saqo ga al’umma. Dalili kuwa shi ne duk lokacin da mawallafin qagaggen labari ya quduri niyyar rubuta labari, farkon abin da yakan zo ransa shi ne maqasudin da zai gina labarinsa a kai.Bayan wannan, abu na gaba shi ne ya yi tunanin ire-iren mutanen da zai qago ya zuba su a cikin labarin waxanda su ne zai yi amfani da su wajen isar da saqonsa ga al’umma. Waxannan qirqirarrun mutane ko aljanu ko dabbobi waxanda mawallafi kan ba su aikin bayar da labari su ake kira taurarin cikin labari. Sau da yawa kuma sukan ture mawallafin wuri xaya su karve ragamar aikin bayar da labari. Su waxannan qirqirarrun taurarin cikin labari waxanda suke karve aikin bayar da labari daga hannun mawallafi, su tsaya a maimakonsa, ma’ana dai su ari bakinsa su ci masa albasa Mukhtar (2004:38) ya kasasu gida biyu, wato mai bayar da labari managarci da kuma mai bayar da labari marar nagarta. Mai bayar da labari managarci shi ne wanda mawallafi ya bayyana shi da cikakken mutum, mai hankali, wanda ba ya qarya da wasu ayyukan assha, don haka, abin da ya ce ko ya faxa

ko ya bayyana a labari za a iya dogara da shi, ba tare da wani xar ba. Shi kuwa mai bayar da labari marar nagarta kishiyar na farko ne.Saboda don haka, duk abin da ya bayyana ba za a iya dogara da shi ba. Manufar wannan takarda ita ce ta bayyana salon da mawallafa qagaggun labarai suke amfani da shi wajen zavin nau'o'in taurarin da suka dace a bigire da muhallai daban-daban wajen isar da saqonsu ga al'umma. Kamar yadda aka yi amfani da su a littafin *Jiki Magayi* na R. M. East da John Tafida Umar Wusasa.

## 1.1 Ma'anar Salo

Salo hanya ce da marubuta suke amfani da ita wajen isar da saqonsu ga al'umma. Masana da dama sun sha kai-kawo game da ma'anar salo, daga cikin su akwai Yahaya da Xangambo (1986:114) inda suka ce "Salo shi ne hanyar da aka bi aka isar da saqon littafi, wato dabarun jawo hankali da sarrafa harshe, misali, amfani da Hausa mai kyau, amfani da kalmomi cikin hikima, gina jumloli da dai sauransu". Shi kuwa Mukhtar (2001:148) ya bayyana cewa "Da wahala a yi farat a ce abu kaza shi ne salo a cikin rubutu. Sai dai abu xaya daga cikin sigoginsa shi ne, salo ya qunshi dabarun jawo hankali ta hanyar sarrafa harshe, wanda kuma ya danganta daga wannan marubuci zuwa wancan". A ganin Sa'id (1978:72) kuwa "Salo shi ne yadda mawaqi ko marubuci ya zana tunaninsa a takarda. Daga nan sai ya duba shi ta ganin shin yana da manufa, kuma bayaninsa yana da qarfi ko rarrauna ne, wato ana fahimtarsa a cikin sauqi ko kuwa sai an yi ta lalube kafin a gane manufarsa". Ita kuwa Bilkisu (2012:9) cewa ta yi "Salo shi ne hanyoyi ko dabarun isar da saqo ga mai ji ko

karantawa, wanda ya kevantu ga mai shi kawai”. Haka ita maAsiya (2012:121) ta bayyana ma’anar salo da cewa "Salo wani wayo ne na yaqar duk wani abu da zai iya kawo tangarxa wajen isar da saqon marubuci. Abin nufi, salo shi ne duk wata kurxa-kurxa da shige da fice da marubuci ya bi domin ya ga haqansa ya cim ma ruwa wajen isar da saqonsa”. Don haka, za a iya bayyana salo da cewa hanyoyi ne da dabaru da hikimomi waxanda marubuta suke amfani da su wajen isar da saqonsa ga al’umma.

## 1.2 Ra’in Dabarun Bayar da Labari

Ra’in Dabarun bayar da labariya qunshi hikimomi da fasahohin da mawallafa qagaggun littattafai na Hausa suke amfani da su wajen isar da saqonsu ga al’umma cikin sauqi. Mukhtar (2004) ya bayyana cewa “Dabarun bayar da labari na marubuci su ne ginshiqan al’amuran da marubuci yakan dogara da su domin ya varje qagaggen labarinsa. Haka kuma dabarun marubuci sun haxar da duk wani irin gwalangwaso nasa da zai iya kawowa kuma a fahimta a cikin labarin (Mukhtar, 2004:34-35). Wannan takarda an xora ta ne a kan ra’in Dabarun Bayar da Labari da Mukhtar (2004) ya samar a littafinsa mai taken *Jagoran Nazarin Qagaggun Labarai*. A cikin wannan takarda za a kalli waxannan fuskoki kamar yadda Mukhtar (2004) ya bayyana:

Taurari
Babban tauraro
Qananan taurari
Tauraro miqaqqe
Tauraro mai gammo
Tauraro mai walqiya

Mai bayar da labari managarci
Mai bayar da labari marar nagarta
(Mukhtar, 2004:38-43 da 68-69)

### 1.2.1 Taurari

Duk lokacin da aka ambaci taurari a fagen nazarin qagaggen labari ana nufin duk ilahirin mutanen ko aljanu ko dai dabbobi da suka tara wata rawa da marubuci ya qirqira ya kuma ba su damar yin magana ko suka aikata wani aiki a cikin labarinsa. Wannan ya nuna ko da dabbobi ma, ko aljanu ya yi amfani da su matuqar ya ba su damar su yi magana, to su ma sun faxa a matsayin taurari, ba lallai sai bil'adam kawai ba. Mukhtar (2004:68) ya bayyana cewa "Taurari su ne ire-iren mutanen da mawallafi yakan sako a cikin labarinsa. Idan suna da yawa, maza da mata, yaro da babba na labarin su ne ake kira taurari, idan kuwa guda xaya ne, to, shi ake kira tauraro.

### 1.2.1.1Nau'o'in Taurari

Kamar yadda aka bayyana a aikin bayar da labari na qagaggen littafi ana samun mutane iri-iri, wasu daga ciki ginshiqai ne, idan babu su to ba labarin, wasu kuma 'yan rakiya ne, suna taimakawa ne don labari ya gudana gaba xaya su ake kira taurari. Sannan a cikin fitattun taurarin ma, wato muhimman akan sami wani daga cikinsu ya fi kowanne shahara a labarin, wannan shi ake kira babban tauraro. Masana da dama sun bayyana cewa taurarin qagaggen littafi sun kasu kashi biyu, wato babban tauraro da qananan taurari, daga cikinsu akwai Galadanci da wasu (1993) da Zarruq da wasu (1996) da

Yahaya da wasu (1992) da Mukhtar (2004) da sauransu. Haka kuma ta fuskar halayya da xabi'ar aiwatarwa, taurari sun kasu biyu, wato mai ba da labari managarci da kuma mai ba da labari marar nagarta (Mukhtar, 2004:38).

Haka kuma, ana fahimtar nau'o'in taurari ta yanayinsu da kuma irin rawar da suke takawa a cikin labarin. Waxannan ire-iren taurari sun kasu gida uku, wato miqaqqen tauraro da tauraro mai gammo da kuma tauraro mai walqiya (Mukhtar, 2004:69). Za a kawo abin da kowanne yake nufi a cikin aikin. Wannan takarda ta mayar da hankali ne kan salon amfani da taurari a matsayin ginshiqin bayar da labari, domin kuwa su ne mawallafa suke dogara da su wajen isar da saqonsu ga al'umma.

## 2.0 Salon Amfani da Taurari a Matsayin Ginshiqin Bayar da Labari a Littafin *Jiki Magayi*

Wannan takarda an yi nazarin yadda mawallafan littafin *Jiki Magayi* suka yi amfani da ire-iren qirqirarrun taurarinsu wajen isar da saqonsu ga al'umma, ta la'akari da nau'o'insu da xabi'unsu da yanayi da kuma irin rawar da suka taka wajen isar da saqon mawallafan ga al'umma. Wannan na nuna gudunmawar da taurari suke bayarwa wajen isar da saqo.Domin idan ba su, ba yadda za a yi mawallafi ya isar da saqonsa ga al'umma.Su yake wakiltawa su bayyana sirrin zuciyarsa, ma'ana su ne suke aron bakin mawallafi su ci masa albasa a lokacin da ya sakar musu aikin bayar da labari. Don haka, yanzu za mu yi nazarin yadda mawallafan littafin *Jiki Magayi*

suka yi amfani da taurari wajen isar da saqon ga al’umma.

## 2.1 Nau’o’in Taurarin Littafin *Jiki Magayi*

Marubutan wannan littafi, wato John Tafida da Umar Wusasa Zariya da R.M. East sun yi amfani da dukkan nau’o’in taurarin littafin qagaggen labari wajen isar da saqonsu ga al’umma kamar haka:

### 2.1.1 Babban Tauraro

Kamar yadda aka bayyana, a qirqirarren littafi ana samun manyan taurari da qanana. Haka kuma a cikin manyan taurarin ma samun xaya daga cikinsu wanda ya fi kowanne shahara a cikin labarin, wannan shi ake kira Babban tauraro. Mukhtar (2004:68) ya bayyana babban tauraro da cewa “shi ne wanda aka gina labarin a kansa, wanda kuma mawallafin yake ta faman tattalinsa, kuma ba ya so wani abu ya same shi a cikin labarin, kuma akasari ma, ko wani abu ya same shi, mawallafin zai yi qoqari ya saqalo labarin yadda reshe zai juye da mujiya, domin a ga cewa shi babban tauraron ya sami nasara”. A taqaice, babban tauraro shi ne wanda ya mamaye kowane saqo da lungu na littafin.Shi ne kuma wanda marubucin yake ba wa saqonsa a hannunsa don ya isar da shi ga al’umma da taimakon sauran taurari.

A littafin *Jiki Magayi* akwai manyan taurari waxanda suka taka muhimmiyar rawa a labarin kamar Zainabu da Malam Shaihu da Tausayinka da sauqi (boka) da Kyauta (Abdullahi xan Malam Shaihu da Zainabu). To amma duk da irin muhimmancinsu a labarin, babban tauraro a litatfin shi ne Abubakar, domin

dukkan labarin ya ginu a kansa, da farko, an bayyana yadda suke soyayya da Zainabu wanda daga baya a sakamakon fassarar mafarkin da aka yi wa Malam Shaihu cewa idan ya aure ta, zai sami magaji, wannan ya sanya da taimakon Malam Sambo ya aure Zainabu.To tun daga lokacin,Abubakar ya ci alwashin ramuwar gayya wanda a sakamakon haka ne duk wasu zirga-zirga da aikace-aikace na littafin suka kasance, sakamako ne na aikin da Abubakar ya aiwatar na neman fansar lahanta kyauta xan Malam Shaihu da Zainabu wanda a qarshe, ya yi nasarar hakan. Don haka, Abubakar shi ne babban tauraron littafin *Jiki Magayi* na John Tafida Umar Wusasa Zariya da R. M. East.

### 2.1.2 Qananan Taurari

Waxannan su ne dukkan sauran taurarin da mawallafin littafin ya qirqira, bayan babban tauraro, waxanda aikinsu shi ne su taimaka wa babban tauraro wajen isar da saqon marubuci ga al'umma, domin su ne waxanda babban tauraro yake taka kafaxunsu ya isar da saqon mawallafi, idan ba domin qananan taurari ba, babban tauraro shi kaxai ba zai iya isar da saqon mawallafi ba. Mukhtar (2004:68) ya bayyana cewa su qananan taurari su ne sauran taurarin da mawallafi bai faye damuwa da abin da zai same su ba a cikin labarin.Daga cikinsu taurarin ana samun mai arziki ko mai karimci, ko matsiyaci ko babban ne na girman jiki ko kuwa yaro ne wanda yawanci mawallafa sukan kawo su ne domin su samar musu wata dangantaka ta musamman da babban tauraro".

Haka kuma su kansu qananan taurarin akwai muhimmai daga cikin, wasu kuma ‘yan rakiya ne domin suna taimakawa ne kawai don labarin ya gudana.Muhimmai daga cikinsu akwai Zainabu da Malam Shaihu da bokaTausayinka da Sauqi wato Zakari da kuma Kyauta, saboda muhimmiyar rawar da suka taka wajen gina labarin, sauran qananan taurari waxanda ‘yan rakiya ne da suka taimaka wajen gudanar da labaran su ne kamar haka Malam Audu (baban Zainabu) da Uwar Zainabu da Malam Sambo da Uban Zakari (wato baban boka Tausayinka da Sauqi) da Aljani mai qaron-kalgo da Uwar Abubakar da Qanin Abubabar da dogon Yaro da alqali da sauransu.

## 2.2 Sauran Nau’o’in Taurari

Bayan nau’in babban tauraro da qananan taurari, akwai wasu nau’o’in taurari kamar yadda Mukhtar (2004:69) ya kawo ire-iren taurari guda uku wato miqaqqen tauraro da tauraro mai gammo da kuma tauraro mai walqiya. Waxannan nau'o'in kashe-kashen taurari an nazarce su a littafin *Jiki Magayi* da yadda mawallafan suka yi amfani da su wajen isar da saqonsu ga al'umma kamar haka:

### 2.2.1 Miqaqqen Tauraro

Miqaqqen tauraro, shi ne wanda da zarar marubuci ya bayyana halinsa, ko da jin sunansa mai karatu ba zai yi mamakin abin da zai aikata ba. A wannan littafi na *Jiki Magayi* an samu miqaqqun taurari da dama kamar haka, Malamin qasa wanda a littafin aka bayyana mana shi ne wanda Malam Shaihuya faxawa

mafarkinsa cewa *"Ya ga wata goxiya a gidan Malam Audu an kai ta kasuwa. Wani mutum yana son ta qwarai da gaske har ya yi ciniki. Sai shi ma ya gan ta ya so ta qwarai ya qara kuxi aka sallama masa, ya biya aka kawo masa gida aka xaure, wancan kuwa ya haqura tilas godiyar kuma ta haifa masa xan duqushi kyakkyawa. Da ya girma ya yi masa sirdi ya hau ya tafi kilisa. Daga can doki ya kada shi ya tsere ya bar shi cikin ciwo qwarai" (Jiki Magayi,* shf. Na 2).

A nan, malamin qasa shi ne ya share qasa, ya buga masa, sannan ya fassara masa mafarkinsa. Haka kuma boka Tausayinka da sauqi, daga jin sunansa ba za a yi mamakin abin da zai aikata ba.A littafin, boka Tausayinka da sauqi shi ne wanda Abubukar ya je wurinsa a garin Zauna-da-shirinka ya bayyana masa abin da yake tafe da shi. Baka Tausayinka da sauqi ya bayyana wa Abubakarcewa, ba isa ce ta sanya Malam Shaihu ya aure masa budurwa ba "*Dalili shi ne yana son xa ne an kuwa gaya masa idan ya auri yarinyar zai samu xa*" (*Jiki Magayi*, shf. na 13). Daga nan sai Abubakar ya buqaci a yi asirin da albarkar da yake nema, ta samun xa, ta zamar masa la'ana. Tausayinka da sauqi ya ce zai yiwu, amma da sharaxin cewa "*Wannan abu zai yiwu, amma da wuya ka yarda in na yi maka dukan hakinsa yana kanka*?" (*Jiki Magayi*, shf. Na 14). Da Abubakar ya yarda, saiboka Tausayinka da Sauqi ya sanya shi ya nemo qaron kalgo, shi kuma ya haxa masa maganin, wanda hakan ya yi sanadiyyar lalacewar Kyauta wanda a qarshe ya kashe mahaifinsa. Don haka ba za a yi mamaki ba, don Boka Tausayinka da sauqi ya haxa wannan magani wanda ya kai ga lalacewar Kyauta har ya kashe

mahaifinsa. Dalili kuwa daga jin sunansa wato Tausayinka da Sauqi, an san ba za a samu jinqai ko tausayi a tare da shi ba. Saboda haka, ya haxo asiri wanda ya yi sanadin lalacewar Kyauta har ta kai ga ya kashe mahaifinsa, wato Malam Shehu ba za a yi mamakin rashin imani da tausayinsa ba.

Haka kuma 'yan fashi waxanda suka yi wa Abubakar fashi a hanyarsata zuwa garin Sanga, inda suka ce da shi "*Kai da ranka da kayanka ka zavi na zava, Abubakar ya ce "Na zavi raina*" (*Jiki Magayi,* shf. na 20). Don haka, daga jin sunansu ba za a yi mamakin abin da suke aikatawa ba. Sannan aljani Mamallakin qaron kalgon haxa mugunta lokacin da Abubakar ya bayyana masa dalilinsa na neman qaron kalgo, Aljanin cewa ya yi, bayan ya qyalqyale da dariya, "*Samari ko da ma mu ba domin alheri ake neman mu ba, sai don mugunta. Da ka zo gare ni tun fari da dukkan wannan wahala ba ta same ka ba, domin mugunta ita ce halina wanda kuma ya yi nufin yin ta shi ne abokina*" *(Jiki Magayi,* shf. na 25)

Bayan haka,Abubakar kansa miqaqqen tauraro ne domin mawallafan sun bayyana Abubakar da cewa mutum ne mai zafin zuciya kamar a lokacin da Abubakar ya fahimci Zainabu ta juya masa baya da ya sanar da mahaifiyarsa, sai ta ba shi haquri. Shi kuwa sai ya ce "*Haba, Iya idan dai ni xan biyu ne, sai na rama, zan shiga duniya ta kowanne hali, na sani Allah zai taimake ni. Amma kada ki damu. Ga Audu nan da qanwata da kakarmu, sun ishe ki zaman duniya, ni kuwa idan da rai wata rana za ki ga na komo"(Jiki Magayi,*shf. na 9). Da ta ji bayaninsa ranta ya vaci qwarai da gaske domin ta

san idan hankalin Abubakar ya tashi ba mai ikon tausan shi. Haka kuma ita ma Zainabu da Abubakar ya fusata, sai ta ce wa Malam Shaihu kamar haka "*Tun da yake Abubakar ya yi zafin zuciyar tasa ina so ka fito zancen neman aure*". *(Jiki Magayi*, shf. na 11). Haka kuma Malam Audu mahaifin Zainabu ya faxa wa Malam Shaihu, Abubakarmai zafin zuciya ne inda ya ce "*Ka sani kuma yaro ne mai zafin zuciya qwarai, idan bai auri Zainabu ba, babu wanda ya san abin da zai yi. Ni ma da kaina ba na fara ba*" *(Jiki Magayi*, shf. na 3).Don haka, ta la'akari da wannan halayya na rashin haquri da zafin zuciya na Abubakar, ba za a yi mamakin yadda aka yi ta ba shi haquri, ya qeqasa qasa ya ci alwashin sai ya rama abin da malam Shaihu ya yi masa na qwace abar qaunarsa, duk da munin abin da zai faru da kuma yadda sakamakon zai koma kansa. Saboda haka, wannan halayya ta Abubakar ta nuna cewa shi miqaqqen tauraro ne.

Sauran miqaqqun taurari a littafin *Jiki Magayi* sun haxar da maharbi da Malam Shaihu da Sarki da Alqali da Malam Audu da Dogon Yaro da Kishiyoyin Zainabu da Akawun kanti da sauransu a sakamakon halayyarsu da kuma rawar da suka taka a labarin.

### 2.2.2 Tauraro Mai Gammo

Tauraro mai gammo shi ne wanda yake da hali gagara koyo. Domin idan ya yi wani hali na kirki ko na taimako a cikin labarin, to wani lokacin sai ya yi abin tsiya, ta yadda za a riqa mamakin anya kuwa shi ne zai aikata haka. Kullum a cikin bayar da mamaki yake. Idan bai yi haka ba, to ba tauraro mai gammo ba ne (Mukhtar,

2004:69). A littafin *Jiki Magayi* na John Umar Tafida Wusasa da R. M. East sun yi amfani da wannan nau’i na taurari. A wannan littafi Zainabu tauraruwa ce mai gammo. Dalili kuwa shi ne qaunar da take tsakaninta da Abubakar ko da wasa ba za a tava kawowa za ta bijire wa Abubakar ba. Domin a lokacin da Malam Shaihu ya kira mahaifin Zainabu Malam Audu ya faxa masa buqatarsa ta neman auren ‘yarsa, sai Malam Audu ya ce:

> “Wannan magana tana da wuya domin kuwa ita Zainabu, tun suna qanana akwaiwani yaro sunansa Abubakar, tare suka taso tana sonsa, shi kuma yana sonta, har kowa ya sani ita zai aura mutane da yawa da samari ba wanda bai zaburo yana sonta ba, amma ta qi sai shi. Shi kuma duk duniyan nan ba ya son kowa sai ita “((*Jiki Magayi*, shf. na 3).

Don a qara tabbatar da irin qaunar da take yi wa Abubakar a lokacin da Malam Shaihu ya tura a kira ta, daga farko cewa ta yi “*Yaro ya koma ya faxa masa ba za ta zo ba*” (Shf. na 4). Haka kuma lokacin da Abubakar ya zo wurinta ransa a vace, don Malam Shaihu ya aika a kira ta, duk da, ba ta je ba hankalinsa ya tashi qwarai, har yake ce mata “*Malam Shaihu attajiri ne, im ba ki so shi don kome ba za ki so shi domin dukiya tasa*” (Shf. na 5). Ita kuma sai ta yi murmushi ta ce da shi “*Haba, Abubakar ai da zai yiwu kuxinsa ake takawa daga nan har mafitar rana babu abin da zai sa in aure shi*” (Shf. na 6). Amma daga baya abin da zai bayar da mamaki shi

ne har ta fara amsa gayyatar Malam Shaihu da Abubakar ya nuna mata rashin amfanin hakan, sai ta ce da shi "*Ai ka sani budurwa haja ce kowa ya gani yana so, kowa kuwa da irin tayinsa, amma mai saye xaya ne ko da ma ba a yi mini baiwa da kai ba, ....*" (Shf. na 9). Wannan ya sanya ya yi fushi, ya tafi abinsa, sannan ya tafi ya shaida wa mahaifinta ya kira ta don ya maganta abin, amma ga mamaki sai Zainabu take cewa "*Ko da an xaure mata Abubakar a qafa, sai ta tsinke, da ta aure shi gwamma ta shiga duniya*" (Shf. na 10). A nan Zainabu ce aka ruwaito ta a matsayinta, ta mai magana ta uku take magana, wanda a qarshe ta auri Malam Shaihu ba Abubakar ba. Haqiqa wannan abin mamaki ne yadda qaunata rikixe ta koma qiyayya. Haka kuma qiyayya ta koma soyayya. Don haka, Zainabu tauraruwa ce mai gammo a labarin.

Sannan Kyauta, wato Abdullahi xan Malam Shaihu da Zainabu tauraro ne mai gammo. Dalili kuwa shi ne, da farko kyauta ya taso da halayen kirki da girmama na gaba da son karatu har ya kusan saukewa, kamar yadda mawallafan suka bayyana shi da cewa "*Tun tasowarsa yaron kirki ne mai nagarta, abin so ga kowa. Kullum abin farin ciki ne ga ubansa, babu irin jin daxin da ba ya jiyad da shi*" (shf. na 18). *Amma daga baya sai ya fara shiririta, ya riqa xauke-xauke da qin zuwa makaranta da qaryace-qaryace, yaro da ko haxa ido da mahaifinsa ba ya yi, amma lokacin da ya ajiye kuxi ya ga bai gan su ba, da ya tambaye shi sai Kyauta ya ce da shi "Ina ruwana, ka ba ni tsaronsu ne*? (Shf. na 31). Wannan ya yi matuqar ba shi mamaki na sauyin halayya kai tsaye. Daga nan abu ya ci gaba, sata wurin Kyauta

kamar vera ga qin zuwa makaranta ga yawace-yawace barkatai ga qin kwana a gida, wannan ya sanya duk gari aka tsargu da shi ana ta mamakin abin da ya faru gare shi kamar yadda mawallafan suka bayyana:

> *"Mutanen gari suka tsargu da shi suna ta mamakin cewa me ya faru? Yaron kirki kamar wannan wanda ba ya iya gai da mutum a tsaye, ba a tava jin ya yi faxa da kowa ba ga shi yanzu ya lalace sai sace-sace kamar vera" (Shf. na 32).*

Haka dai abu ya ci gaba ga Kyauta kullum munanan halaye sai yawaita suke kullum a jawo wa iyayensa magana da zunxensu ake wanda a qarshe, suka yanka shawara suka bar garin, wato mahaifinsa Malam Shaihu da mahaifiyarsa Zainabu suka koma Garin Garuje inda ba wanda ya san su. Allah ya albarkaci nomansa har ya zama yana daga cikin manyan masu arzikin garin. A wannan gari ne kuma Kyauta da abokinsa na sata, wato Dogon Yaro suka haura gidan Malam Shaihu da niyyar yin sata, wanda a qarshe, Kyauta suka kama kokawa da mahaifinsa har ya kashe mahaifinsa nasa. A sakamakon haka, Kyauta tauraro ne mai gammo ganin yadda ya taso a matsayin yaro na gari, canjin halayyarsa daga na gari zuwa abin tsiya ya ba wa kowa mamaki.

### 2.2.3 Tauraro Mai Walqiya

Tauraro mai walqiya shi ne tauraron da mawallafi ya sako shi a cikin labari ba tare da ya qaddamar da shi ba ga mai karatu, sannan kuma mawallafi yakan janye shi, ba tare da ya sanar da mai karatu ba (Mukhtar, 2004:69). Waxannan nau'i na taurari masu walqiya yawanci 'yan rakiya ne domin suna taimakawa ne kawai don labari ya gudana. Waxannan marubuta sun yi amfani da irinwaxannan taurarin a littafinsu na *Jiki Magayi* kamar haka. Misali Yaron mai gida, wato yaron Malam Shaihu, shi ne wanda Malam Shaihu ya aike shi tun farko gidan su Zainabu ya kira ta, sannan shi ne wanda ya kai wa Abubakar labarin uban gidansa yana son Zainabu, daga nan kuma mawallafan suka janye shi ba tare da sun sanar ba. Haka kuma qanen Zainabu wanda lokacin da Abubakar ya je gidan su, ya aike shi ya kira Zainabu daga nan kuma mawallafin ya janye shi.

Sannan lokacin da Abubakar ya zo garin Zauna-da-shirinka, sai ya sami gindin bishiya ya kwanta, har bacci ya xauke shi. Mutumin da ya zo ya tashe shi daga bacci ya tambaye shi "*Samari daga ina kake"* (shf. na 11) bayan ya bayyana masa daga inda yake da buqatarsa na haxuwa da wani boka, shi ya yi masa kwatancen gidan boka Tausayinka da sauqi, wanda daga nan kuma mawallafan suka janye shi. Haka kuma 'yangadi waxanda a lokacin da Kyauta ya zo kano da daddare, bayan kowa ya yi bacci da dare sai ya fita yawon sata ya shiga wani gida suna ganinsa suka yi masa tara-tara suka kama shi da kayan sata niqi-niqi. Ya jefar zai gudu 'yan gadin suka kama shi, suka tafi da shi gidan Sarkin gadi

ya kwana. Da gari ya waye aka kai Kyauta gidan alqali aka xaure shi shekara biyu. To su ‘yangadin taurari ne masu walqiya domin tun daga lokacin da aka janye su ba a sake komawa ta kansu ba har aka kammala labarin domin dama an sako su ne ba tare da an qaddamar da su ba, aka kuma janye su ba sallama. Haka kuma Doguwa, wato aljanar Tausayinka da sauqi wadda ta bayyana wa Tausayinka da sauqi abin da Abubakar yake tafe da shi kamar yadda Tausayinka da sauqi yake bayyana wa Abubakar "*Dukan abin nan da ya kawo ka kafin ka faxi na rigaya na san shi. Domin jiya bayan da muka rabu Doguwata zo ta bayyana mini dukkan abin nan da yake tafe da kai*" (Shf. na 12) tun daga nan sai mawallafan suka janye ta.Shi ma aljani mamallakin Qaron kalgo da ya tsorata Abubakar wanda a qarshe kuma ya ba shi qaron kalgo, shi ma tauraro ne mai walqiya, domin mawallafan suna sako shi ne don ya taimaka labarin ya gudana suka kuma janye shi.

Har ila yau, sauran taurari masu walqiya da mawallafan suka yi amfani da su a labarin sun haxar da qanen Abubakar Audu da qanwar Abubakar da kakar Abubakar da matar da Kyauta ya gamu da ita a lokacin da ya je gidan Abubakar xaukan fansa da maharbi da uwar Zainabu da uwar Abubakar, dukkansu taurari ne masu walqiya a labarin, domin mawallafan sun sako su ne ba tare da qaddamar da su ba, sai don labarinsu ya tafi daidai ba tare da yankewa ba, sannan kuma suka janye su ba tare da sun sanar ba, sai dai kawai aka rufe babin su da sauransu.

## 2.3 Nagartar Taurari

A wajen aikin bayar da labari musamman masu bayar da da labari daga cikin fage, wato qirqirarrun taurarin marubuci waxanda yake sakar wa aikin bayar da labari su tsaya a maimakonsa, ma'ana dai masu aron bakin mawallafi su ci masa albasa. Mukhtar (2004:38) ya bayyana cewa "Waxannan taurari iri biyu ne, wato akwai mai bayar da labari managarci da kuma mai bayar da labari marar nagarta. A littafin *Jiki Magayi* mawallafan sun yi amfani da ire-iren waxannan taurari kamar haka:

### 2.3.1 Mai Bayar da Labari Managarci

Wannan shi ne tauraron da mawallafi ya bayyana shi da cewa shi cikakken mutum ne, mai hankali wanda ba ya qarya, ba ya kuma wasu ayyuka na assha. Don haka, idan ya bayar da wani bayani game da wani al'amari, za a iya dogara da abin da ya faxa, ba tare da an yi wani xar-xar ba (Mukhtar, 2004:38) mawallafan wannan littafi sun yi amfani da ire-iren salon waxannan taurari a littafinsu kamar haka: Malam Shaihu tauraro ne managarci, domin mawallafan sun fito da shi cikin sigar mutum kamili mai gaskiya, mai karamci kuma nutsattse, don haka, dukkan abin da ya faxa za a iya yarda a kuma dogara da shi, ba tare da wani xar-xar ba. Bayan malam Shaihu Malam Audu mahaifin zainabu shi ma tauraro ne managarci domin an bayyana shi da mutum ne mai gaskiya, karimi kuma mai cika alqawari, domin a lokacin da Malam Shaihu ya yi kiransa game da maganar auren 'yarsa Zainabu, duk da cewa ya san Malam Shaihu mawadaci ne, sai da ya faxa masa gaskiya cewa Abubakar yana son ta, kuma ita ma tana son sa kamar yadda Malam Audu ya ce "*Wannan magana tana da*

*wuya domin Zainabu tun suna qananan akwai yaro mai suna Abubakar tare suka taso suna qaunar juna, har kowa ya sani, ita zai aura domin mutane da yawa da samari sun bijiro suna son ta, amma ta qi kowa sai shi. Shi kuma duk duniya ba ya son kowa sai ita*" (Shf. na 3). Haqiqa idan ba don gaskiyarsa ba, ko domin dukiyar Malam Shaihu amincewa zai yi. Sannan a lokacin da Abubakar ya fahimci sauyi tsakaninsa da Zainabu ya kai qara wajen mahaifinta Malam Audu a nan Malam Audu cewa ya yi da Abubakar "*A inaka ji wannan maganar banza? Dattijo irina zai yi magana biyu? Idan ni na haifi Zainabu, to ba ta da miji sai kai*" (Shf. na 10).Duk da cewa Abubakar bai auri Zainabu ba, mahaifinta Malam Audu ya tabbatar da dattijo ne domin an yi auren ba tare da so ransa ba, don haka Malam Audu tauraro ne managarci waxannan da wasu dalilai su suka tabbatar da cewa Malam Audu tauraro ne managarci.

Sauran taurari managartamasu bayar da labari sun haxar da Sarkin garin Galma da na garin Garuje da Alqali.Marubutan sun bayyana su da cewa mutane ne masu faxa a ji, masu gaskiya da karamci, kuma nutsattsu waxanda ba sa qarya, waxanda mutane suka dogara da su wajen warware matsalolinsu, don haka duk abin da suka faxa a labarin, abin da za a iya dogara da shi ne ba tare da wani xar-xar ba da dai sauransu.

## 2.3.2 Mai Bayar da Labari Marar Nagarta

Wannan kishiyar mai bayar da labari mai nagarta ne, domin yana qarya da munafunci da tayar da zaune

tsaye, ba kamili ba ne, sannan ba nutsattse ba ne. Don haka, duk abin da ya faxa ba za a dogara da shi ba. Waxannan mawallafa sun yi amfani da irin waxannan taurari a cikin littafinsu na *Jiki Magayi*. Misali Boka Tausayinka da sauqi da Dogon Yaro (Babban varawo) da ‘yan fashi da aljani mamallakin qaron kalgo da doguwa, aljanar boka Tausayinka da sauqi, dukkansu taurari ne marasa nagarta, domin a labarin sun nuna maqaryata ne su. Masu mugunta kuma mazambata, misali Dogon Yaro a labarin qasurgumin varawo ne kuma yana tafiye-tafiye da yawace-yawacen satarsa har ya gamu da Kyauta ya koya masa neman laqanin sata da damfara. Don haka, duk lokacin da aka ba shi damar bayar da labari duk abin da ya faxa, an san mai bayar da labari marar nagarta ne da dai sauransu.

## 3.0 Qalailaicewa

Salon zavin taurari abu ne muhimmi a cikin aikin bayar da labari, domin ta hanyar amfani da taurarin ne mawallafa suke samun damar isar da saqonsu ga al’umma cikin sauqi. A wannan takarda, an gano cewa marubutan littafin *Jiki Magayi* sun yi amfani da salon zavin sunayen mutane da aljanu a matsayin qirqirarrun taurarinsu, domin su tafi daidai da yanayin tsarin rayuwa ta zahiri yadda za ta dace da irin ta ‘yan’adam. Wannan ya sanya ba su yi amfani da dabbobi da tsuntsaye ba wajen ba su aikin bayar da labari, a matsayin qirqirarrun taurarinsu kamar yadda yake a salon zavin taurarin wasu mawallafan.

Sannan mawallafan littafin *Jiki Magayi* sun gina saqon labarinsu ne a kan wasu abubuwa da za a iya

kwatanta su da rayuwa ta zahiri, domin a rayuwar yau da kullum ta Hausawa ba abin mamaki ba ne don wani ya yi wa wani asiri a sakamakon neman aure, ko mai hannu da shuni ya qwace wa talaka matar ko budurwar da zai aura ko ma wani ya kashe wani a zahiri ko ta hanyar asiri wajen neman aure, ko nuna rashin haquri da fita neman xaukar fansa. Wannan ya yi daidai da karin maganar Hausawa da ake cewa "Ramuwar gayya, ta fi ta gayya zafi". Ko "Rama cuta ga macuci ibada" da sauran ire-irensu. Wannan ya sanya wajen samar da taurarinsu, suka qirqiri waxanda za su dace da abin da yake faruwa a rayuwa ta haqiqa, duk da cewa ba wai lallai sun tava wanzuwa a zahiri ba. Don haka, mawallafan sun samar da taurarinsu ne kawai a cikin duniyar tunani irin tasu kuma suka ba su darajoji daban-daban dangane da qirar jiki, kwarjini, cika-fuska ko akasin haka da sauransu. A taqaice dai, a rayuwa ta zahiri suka gina labarinsu ba a kan tatsuniya ko almara ba, wanda hakan ya yi tasiri wajen samar da qirqirarrun taurarinsu.

Bugu da qari, binciken ya gano cewa fahimta da hikima da dabarun mawallafa ba su zama iri xaya ba, wannan kuwa yana faruwa ne a sakamakon bambancin ilimi da gwagwarmaya da gogewa da zirga-zirgarsu wanda hakan kan yi matuqar tasiri wajen samar da taurarinsu.

Haka kuma an gano cewa mawallafan littafin *Jiki Magayi* sun yi amfani da dukkan nau'o'in taurarin qagaggen labari tun daga kan babban tauraro da qananan taurari da sauran nau'o'i kamar tauraro mai gammo da miqaqqen tauraro da tauraro mai walqiya da kuma nau'in taurarin da akan samu ta fuskar halayya wato tauraro mai

bayar da labari da managarci da kuma mai bayar da labari marar nagarta. Wannan ya sanya a sakamakon wannan bincike, ana iya fahimtar cewa Ra'in Dabarun Bayar da Labari da Mukhtar (2004) ya samar ya dace da nazarin ire-iren hikimomi da fasahohin da mawallafa qagaggun labarai na Hausa suke amfani da su wajen isar da saqonsu ga al'umma. A qarshe, mawallafan sun yi amfani da sassauqan salo wajen samar da taurarinsu da yanayin maganarsu a lokacin da suka ba su aikin bayar da labari da aiwatar da aikinsu da kuma yanayin mu'amalarsu da sauran taurari 'yan'uwansu a cikin labarin wanda hakan ya tallafa wajen isar da saqonsu a cikin sauqi ga al'umma.

## 3.1 Kammalawa

A wannan takarda an yi bayani a kan salon zavin taurari da marubuta qagaggun littattafai suke amfani da su wajen isar da saqon su a matsayin ginshiqin isar da saqo, an bayyana cewa tun farko idan marubuci ya qudiri niyyar rubutu, bayan maqasudin rubutun, abu na gaba shi ne ya yi tunanin ire-iren qirqirarrun taurarin da zai yi amfani da su wajen cim ma manufarsa. Sannan takardar ta yi waiwaye game da gudunmawar masana kan ma'anar salo da nau'o'in taurari, sannan daga nan ne takardar ta mayar da hankali kan yadda marubutan littafin *Jiki Magayi* suka yi amfani da salon zavin taurari wajen gina labarinsu.

Sannan a takardar an fahimci cewa su kansu taurarin nau'i-nau'i ne, bayan babban tauraro da qananan taurari,akwai kuma tauraro mai gammo da miqaqqe da kuma tauraro mai walqiya.Ta fuskar halayya kuwa,akwai

tauraro mai bayar da labari maganarci da kuma mai bayar da labari marar nagarta, wanda wajibi ne marubuci ya yi zuzzurfan tunani wajen zavinsu da ba su darajojin da suka dace da su, kamar qirar jiki da cika fuska da kwarjini ko akasin haka, ta hanyar bayani da kwatance da yanayin maganarsu da aiwatar da aiki da kuma mu'amalarsu da sauran taurari 'yan'uwansu a cikin labarin, da sauransu.

Haka kuma a takardar anaiya fahimtar cewa Ra'in Dabarun Bayar da Labari da Mukhtar (2004) ya samar ya dace da nazarin ire-iren hikimomi da fasahohin da mawallafa qagaggun littattafai na Hausa suke amfani da su wajen isar da labarinsu ga mai karatu cikin sauqi. Sannan a qarshe, jawabin kammalawa ya biyo baya aka kuma taqaita sakamakon bincike. Sai kuma manazarta ta biyo baya.

## Manazarta


Asiya,M. N. (2012) "Magana Jari Ce (1-3) "Nazarin Salo da Sarrafa Harshe". Kundin Digiri na Uku. Kano: Jami'ar Bayero.

Bilkisu, Y. H. (2012) "Kwatanta Salon Rubutun Bilkisu Ahmad Funtuwa da Bilkisu Yusuf Ali a Ma'aunin Harshe". Kundin digiri na Uku. Kano: Jami'ar Bayero.

East, R. M. da Tafida, J. U. (1933) *Jiki Magayi* . Kaduna:Hukumar Talifi.

Galadanci, M.K.M. da wasu (1993) *Hausa Don Qananan Makarantun Sakandare Littafi na 3*. Longman Nigeria Plc. Ikeja, Lagos.

Mukhtar, I. (2001) “Al’amuran Dubawa Cikin Nazarin qirqirarrun Littattafai” a cikin *Algaita: Journal of Current Research in Hausa Studies. Bugu na I,* Lamba ta I. Kano: Jami’ar Bayero.

Mukhtar, I.(2004) *Jagoran Nazarin Qagaggun Labarai Tsari na Biyu*. Kano: Benchmark Publishers Nig. Ltd.

Sa’id, B. (1978) “Salo a Tsarin Rubutacciyar Waqar Hausa”. Takardar da aka Gabatar a Taron Qara wa Juna Sani na Farko, wanda Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya ta shirya. Kano: Jami’ar Bayero.

Yahaya, I. Y. da Wasu (1992) *Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare*. Littafi na Xaya. Ibadan: Univertsity Press Plc. Nig. Ltd.

Yahaya, I. Y. da Xangambo, A. (1986) *Jagoran Nazarin Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare*. Zaria: N.N.P.C. Nig. Ltd.

Zarruq, R. M. da wasu (1996) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Qananan Makarantun Sakandare Littafi na Biyu*. Ibadan: University Press Plc. Nig. Ltd.